Shi ruwansa mai tsarkakewa ne, kuma mushensa halal ne

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Wani mutum ya tambayi Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, sai ya ce: Ya Manzon Allah, mu muna tafiya a teku, kuma muna ɗaukar ruwa kaɗan tare da mu, idan muka yi alwala da shi zamu ji ƙishirwa, shin zamu yi alwala daga ruwan kogi? sai Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Shi ruwansa mai tsarkakewa ne, kuma mushensa halal ne".

[Ingantacce ne] [Abu Dawud da Tirmizi da Nasa'i da Ibn Majah da Ahmad ne Suka Rawaito shi]

Wani mutum ya tambayi Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - sai ya ce: Lallai mu muna hawa jiragen ruwa a cikin kogi dan sū ko kasuwanci da abinda ya yi kama da hakan, kuma muna ɗaukar ruwa kaɗan wanda za'a iya sha, idan muka yi anfani da ruwan shan dan yin alwala da wanka zai ƙare, kuma ba zamu samu wanda zamu sha ba, shin ya halatta garemu mu yi alwala da ruwan kogi? Sai tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce game da ruwan kogi: Ruwansa mai tsarki ne kuma mai tsarkakewa; alwala tana halatta da shi da kuma wanka da shi, kuma halal ne cin abinda yake fita daga cikinsa na kifaye da wasunsu, koda an samu mushe ya fito a bayansa ba tare da an yi sū dinsa ba.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/8355